# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da



# Samaniya, kyakkyawar gidan ubangiji

**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Sarah S.**

**Fassarawa: Maren Dameng Daniel**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2020 Bible for Children, Inc.**

**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**

**Lokacin da Yesu na duniya, ya fadawa almajiransa game da samaniya yana kiransa “Gidan ubana,” ya kuma ce akwai wurin zama dayawa. Gidajen manya-manya ne kyakkyawu. Samaniya nada fadi da kuma kyau fiye da dukan gidaje na duniya.**



**Yesu yace “zan je in shirya muku wuri, idan na gyara muku wuri zan sake dawowa don in kai ku wurin na.” Yesu ya tafi sama bayan ya tashi daga matattu.  Yayin da almajiransa suna jira suna kallo, aka ɗauki Yesu, sai ya bace a cikin giza-gizan sama, basu sake ganinsa ba.**



Tun daga wancan lokali, mabiyan Yesu su na tuna alkawarin Yesu na zuwa ya dauke su. Yesu ya ce 'Zai dawo da wuri' a lokalin da bamu zata ba. Amma Kiristan daya mutu kafin ya dawo fa? Littafi ya ce za su tafi su zauna da Yesu. A mutu a jiki shi ne a kasance da Allah.



**Wahayi, littafi na ƙarshe a cikin littafi mai tsarki, ya bayyana mana yadda Fasari da kyawun samaniya take. Wani babban abu shi ne, samaniya gidan Allah ne. Allah yana ko ina amma kursiyinsa na can a sama.**



**Mala'iku da dukkan halittun sama suna sujada ga Allah a samaniya. Haka nan duk wadanda suka mutu suka tafi sama. Suna raira waka na musamman na yabon Allah.**



**Ga wasu kalamai daga waƙa da suke rairawa: KA CANCANTA DON KA YI CETON MU DA JININKA DAGA KOWANE ƘABILA DA ƘASA SAI KA MAISHE MU SARAKUNA DA LIMAMAI GA ALLAH MU (WAHAYI. 5:9)**



**Fallen ƙarshe na littafi mai tsarki ya kwatanta samaniya kamar "sabuwar urishalima." Yana zama babbane sosai da Katanga mai tsayi a wajensa. Bangon anyi da duwatsu masu daraja ne masu walkiya.**



**Duwatsu masu daraja sun rufe duwatsu da aka yi tubalin ginin suna dauke da launuka mai kyau da walkiya. Kowacce babban kofa na birnin, an yine da duwatsu manya-manya masu daraja.**



**Waɗannan kofofin masu walkiya ba'a kullewa. M’ushiga ciki mu duba ...kaii!  Samaniya tafi kyau ta ciki.  Birnanen anyi ne da zallar zinariya kamar kwalba mai walkiya.  Hanyoin samaniya anyi shi da zinariya ne.**



**Kyakkyawan rafi na sabtacciyar ruwan rai na gudanya daga kursiyin Allah.  A gefen rafin ruwan rai din akwai itaciyar rai wadda aka fara samun ta a gonar Eden. Wannan itaciyar na musamman ne.  Tana haihuwan 'ya'yaye daban daban guda goma sha biyu, kowane iri a kowacce wata.  Kuma ganyayya kin wannan bishiya amfaninsa shi ne warkar da ƙasashe.**



**Samaniya bata buƙatan rana ko wata domin ta haskaka. Ɗaukakan Allah da babban wuta mai haske ya cika samaniya.  Babu dare ma a can.**



**Dabbobin samaniya ma, dabban ne. Ba sa gaba da mutane suna zaman fahimta da abota ne. Kuraye da raguna abincinsu ciyawa tare. Ko manyan zakuna ma suna cin ciyayi kamar shanu. Ubangiji ya faɗa “Ba za su ɓata wani abu ba ko su hallaka kowa ba a tsauni na mai tsarki.”**



Yayin da muka duba mun tarar akwai ababan da babu a samaniya. Babu kalaman fushi, ba wanda ke yin faɗa ko nuna son kai. Babu wani kwaɗo a kan ƙofofi don babu barayi a samaniya.



Babu makaryata, masu kisan kai da sauran mugayen mutane. Babu wani abu da yake zama zunubi a samaniya.



A samaniya wurin Allah babu hawaye. Wani lokaci Mutanen Allah suna kuka don baƙin ciki na wannan rayuwa. A samaniya Allah zai share dukkan hawaye.

Babu mutuwa a samaniya ko kadan. Mutanen Allah za su kasance da Allah har abada. Babu damuwa, babu kuka, babu jin zafi. Babu ciwo babu rabuwa, babu yin biso. Kowa a sama zai zauna cikin farin ciki da Allah har abada.



**Wani babban abu shine, samaniya na samari da ‘yanmata ne, da (iyaye da tsotsofi ma) wadanda suka gaskata da Yesu a matsayin ubangiji mai cetonsu kuma suka yi biyayya ga ubangijin su.  A cikin samaniya akwai wani littafi mai suna littafin rai na ɗan rago.  Yana cike ne da sunayen mutane. Ka san sunayen waɗanda aka rubuta a cikin littafin rai?  To waɗanda suka bada gaskiya ga Yesu ne.**

**Sunanka yana ciki?**



Kalmar karshe a cikin littati mai-tsarki game da samaniya wata kyakkyawan kira ne da gayyata. “Da ruhu da Amarya suka ce 'Zo!' Duk wanda yaji sai yace 'Zo!' Duk mai ƙishi yazo.  Kuyi abun da kuke so kusha ruwan rai kyauta.”



**Samaniya, kyakkyawar gidan ubangiji**

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Yahaya 14;**
**2 Korintiyawa 5,**
**Wahayi 4, 21, 22**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16